


An yi wani maharbi.


Ba ya farautar wata

dabba sai jaki.



Wata rana maharbi ya koro wani jaki.


Jaki ya shiga gidan doki.



Jaki ya na son wuri ya ɓoye.

Doki ya kai jaki a ɗaki.

Jaki ya yi murna.



Ashe doki na shirin

munafurci.

Doki ya sa yaransa su

tare kofa.

Jaki ya kwanta a ɗaki.



Doki ya shiga daji.


Ya je neman maharbi.



Doki ya sami marhabi.


Ya faɗa masa inda jaki

ya ɓoye.



Marharbi ya je gidan doki.

Marhabi ya ga yaran doki a kofa.



Yaran doki sun fi jaki kyau.

Marharbi ya fasa farautar jaki.

Ya shiga farautar doki.